1.10a

# LOKACI DA SALLA

## MAZA

**Bàlā:** Bā̀bankà yanā̀ nan?

**Yārṑ:** Ē, iyā̀ gidā, àmmā baccī yakḕ.

**B:** Baccī yakḕ yî?

**Y:** Ē.

**B:** Tô, kà cê à tāsō shì.

**Y:** Tô.

*Yārṑ yā shìga gidā, Bàlā dà John sukà dākàtā. Bāyan lōkàcī kàɗan, sai ya fitō.*



**Y:** Bā̀ba yā cê kù shigō.

**John:** Zō. *Yārṑ yā tahō wurinsà.* Mḕ ya cḕ?

**Y:** Bā̀ba yā cê kù shigō.

**John:** Tô. **Bàlā:** Mḕ ya cḕ?

**Y:** Bā̀ba yā cê kù shigō.

**B:** Tô.

**J:** Mù jē.

*Sun bi yārṑ sun shìga gidā.*

**J:** Sàlāmù àlaikùm.

**Ā̀hmadù:** Wà àlaikùm sàlāmù.

*Sun tūɓḕ tā̀kàlmī sun zaunā̀.*

**Ā̀madù:** Bar̃kànkù dà zuwā̀.

**Bàlā:** Ǎ, bar̃kā̀ kàdai.

**A:** Mālàm Bàlā?

**B:** Ìnā gàjiyā̀?

**A:** Dà kai dà Mālàm John nē?

**B & John:** Ē. (Bàlā) Mū biyu nḕ.

**A:** Sànnunkù dà zuwā̀.

**B & J:** Ē, sànnu kàdai.

**A:** Yâwwa!

**B:** Yā̀ nā ga fuskā̀r̃kà nēnḕ nē. Kai lallē kùwa dà àlāmā̀ àkwai bacci à idònkà.

**A:** Ai nā shā baccī.

**B:** Kā shā baccī?

**A:** Kwar̃ai kùwa!

**B:** Lallē kā shā baccī. ... Yànzu ka tāshì?!

**A:** Ā'ā̀, nā tāshì tun ƙarfḕ bìyar̃ dà rabì̀ nā yi sallàr̃ àsùbâ. Sànnan sai na kōmā̀ na kwântā.

**B:** Tô [Ē] ... tô, lallē kā shā baccī, [Hakà nē] ... lallē kā shā baccī [hakà nē].

**A:** Yā̀yā̀ gàrī?

**B:** A, àlhamdù lìllāhì!

**A:** Ap! Ai kò yā kàmātà yànzu ìn tāshì ìn yi sallàr̃ àzahàr̃ dòmin lōkàcī yā yi.

**B:** Yànzu ƙarfḕ nawà?

**A:** Yànzu ƙarfḕ ɗaya dà rabì̀. [Tô] Kù yi jirā̀nā ìn yi sallā̀.

**B:** Tô, bâ dā̀muwā.

*Yā sōmà sallā̀.*

**John:** A, Ā̀madù, bā̀ ni ruwā ìn shā. ... Ā̀madù, bā̀ ni ruwā ìn shā!

**B:** John!



**J:** Nà'am?

**B:** Habà, John! Bā ā̀ yi wà mài sallā̀ màganā̀!

**J:** Ā̀hâ! Bàn sanì̀ ba.

**B:** Bā ā̀ yi wà mài sallā̀ màganā̀.

**J:** Tô! Tò̀ mādàllā!

*John yā tāshì yā wucḕ gàban Ā̀hmadù wandà yakè̀ cikin sallā̀ yā ɗēbō ruwā yā shā yā dāwō.*

**J:** Nī nā ɗēbō dà kâinā.

**B:** John!

**J:** Ě?

**B:** Bā à̄ bî ta gàban mài sallà̄.

**J:** Ā'ā! Tô, bā à̄ bî?!

**B:** Ē, in mùtûm yanā̀ yîn sallà̄, bā à̄ bî ta gàbansà.

**J:** Tô, zân iyà bî ta bāyansà?

**B:** Yâwwa! Zā kà iyà bî ta bāyansà.

**J:** Tò̄ mādàllā.

**B:** Ta bāyansà kawài zā kà biyō.

**J:** Tô, tò̄ nā gōdè.

**B:** Mādàllā.

**A:** *Yā īdà sallà̄.* Sàlāmù àlaikùm, wà rahàmatù-llah. Sàlāmù àlaikùm, wà rahàmatù-llah. *Yā jūyā̀ wajen bā̀ƙī.* Am, sànnunkù.

**B & J:** Yâwwa, sànnu kàdai.

**A:** Yâwwa.

**B:** Kā gamà sallà̄?

**A:** Àlhamdù lìllāhì?

**B:** Tô, mādàllā.

**J:** Mālàm Ā̀madù ...

**A:** Mālàm John.

**J:** Nī bàn san bā à̄ wucè̄ ta gàba ba. [Ē] Yi hàƙurī! Nā ɗēbō ruwā nè̄.

**A:** Ē tò̄, ai shī kè̄ nan. Dâ mā rashìn sanī̀ ne. [B: Yâwwa] È̄, dâ mā shī ya sâ Mālàm ... nā ji mā lōkàcîn dà Mālam Bàlā yakè̄ gayā̀ mâ [J: Tò̄ mādàllā.] cêwar̃ bā à̄ wucè̄ ta gàban mài sallà̄.

**J:** Tò̄ ai kuma nā yi makà màganā̀. Bâ kōmē?

**A:** Ā'à̄, ai dâ mā mài sallà̄, bā à̄ yi masà màganā̀.

**J:** Tò̄ shī kè̄ nan.

1.10b

# LOKACI DA SALLA

## MATA

**Bintà:** Sàlāmù àlaikùm.

**Hajàr̃ā:** Wà àlaikùm às-sàlâm. ... A'a, Bintà cē?

**B:** Ī, nī cè̀.

**H:** Sànnu dà zuwà̀.

**B:** Yâwwa! Ìnā wunì̀?

**H:** Lāfiyà̀ lau.

**B:** Ìnā gàjiyà̀?

**H:** Bâ gàjiyà̀.

**B:** Yà̀ yârā?

**H:** Yârā lāfiyà̀ ƙalau.

**B:** Tò̀ mādàllā.

**H:** Ap! Bàn yi sallàr̃ [sallàl] lì̀shā ba. Bàri ìn tāshì ...

**B:** Har̃ yànzu bà kì yi sallàr̃ [sallàl] lì̀shā ba?!

**H:** Wàllāhì, bàn yi ba. Inà̀ ta hidimar̃ [hidimag] gidā. Ɗan jìrà̀ ni don Allà̀h.

**B:** Tò̀ shī kè̀ nan, bàri ìn jirā kì.

*Hajàr̃ā tā yi sallà̀.*

**H:** As-sàlāmù àlaikùm. ... As-sàlāmù àlaikùm.



**B:** Har̃ kin idar̃?

**H:** Wàllāhì nā idar̃. Bàri mù ƙārà gaisà̀wā, kō?

**B:** Tò̀ ìnā wunì̀?

**H:** Ìnā gàjiyà̀?

**B:** Bâ gàjiyà̀.

**H:** À̀lbishì̀r̃inkì!

*Sun tāfà̀.*

**B:** Gōr̃ò!

**H:** Farī kō jā?

**B:** Farī!

**H:** Gùdā kō ɓārī̀?

**B:** Gùdā nakḕ sô!

**H:** Kin ga tsàrabàr̃ dà mijī̀nā ya kāwō minì dàgà hajī̀.

**B:** Kai kai, kai kai, kai! Ā̀mmā yanā̀ dà ɗan kàren kyâu!

**H:** Kē dai bà kì ga ba. Nī mā nā yi mur̃nā̀ dà shī.

**B:** Gaskiyā yanā̀ dà kyâu. ... Tô, nī dai bàri ìn tāshì ìn tàfi.

**H:** Har̃ zā kì tàfi?

**B:** Ē, zân tàfi. Sai an kwāna biyu.

**H:** Tṑ kì gai dà gidā. Sai an kwāna biyu kḕ nan.

**B:** Gidā yâ ji.

*Hajàr̃ā tā bi Bintà har̃ zuwā̀ ƙōfā̀.*

**H:** Kì gai dà gidā, kō?

**B:** Tṑ gidā yâ ji.